# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na goma: Bayan wuya sai daɗi

Wanda ya rubuta: James Muhando
Wanda ya fassara: Danlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Mai ba da labari: | ɗan shekara 30 |
| Kwastoma | |
| Kawu Natanko: | ɗan shekara 45 |
| Ali: | ɗan shekara 15 |
| Mai ciniki: | 'yar shekara 30 |
| Babawo | |
| Maman Ladi: | 'yar shekara 40 |
| Bash: | ɗan shekara 15 |

**Mai ba da labari:**

Masu saurare, barkanmu da sake saduwa da mu a cikin shirin namu na "Ji Ka Karu". Wannan shi ne kashi na goma kuma na ƙarshe a cikin wasan kwaikwayonmu mai suna "Aljannar Kare – Haɗarin Afkawa Cikin Bashi". Kada dai ku manta, sunana Aliyu Bello, ni ne jami'in bayar da basussuka a banki kuma jagoran shirin.

A yau zan ɗauke ku ne zuwa ɗan ƙauyen nan namu. Yanayin ƙauyen da kuma iskar da mutum kan shaƙa mai daɗi abin ba magana. Af, ai ga Kawu Natanko can ma a cikin kantinsa na kayan marmari. Ku biyo ni mu je, Allah Ya sa dai jarin nasa bai karye ba.

**Fitowa ta 1: A wurin sayar da kayan marmari na Kawu Natanko**

**Kwastoma:** Gaskiya kam Natanko, lemon nan naka da zaƙi. Ko za ka ɗan ƙara mini?

**Kawu Natanko:** Me zai hana!

**Ali:** Kawu Natanko ina kwana?

**Kawu Natanko:** Lafiya lau. A zo a duba, muna sayar da kayan marmari iri-iri, akwai mangwaro, akwai lemo, … Au, ashe ma Ali ne, zo mana! Wato zolayata kake ko? Ko kuma dai so kake ka sa min ciwon zuciya? Wallahi na ɗauka wani kwastoma ne ba kai ba!

**Ali:** Kai kuwa Kawu, me zai sa ka samu ciwon zuciya? Ko har yanzu akwai masu binka bashi ne da kake guje wa?

**Kawu Natanko:** Zo don Allah, zo ka rungume ɗan tsohon nan! Yaya dai ɗana, kana lafiya ko?

**Ali:** Garau kuwa.

**Mai ciniki:** Kawu Natanko! Ina son kilo biyu na ayaba, da kilo biyu na lemo, da kuma kilo biyu na mangwaro!

**Kawu Natanko:** Maman Salim, ina kwana! Kika ce kilo biyu na ayaba, da kilo biyu na lemo, da kuma kilo biyu na mangwaro, ko? Yauwa! To kuɗin ya tashi Dala huɗu ke nan.

**Mai ciniki:** To ga shi! Na gode.

**Kawu Natanko:** A gai da gida. … Kai dai zauna kawai! Faɗi abin da zan ba ka, lemo ko mangwaro?

**Ali:** Haba Kawu, ai ka san na fi son mangwaro!

**Kawu Natanko:** To mantuwar kuma fa, ba ka san tsufa ke ci min dunduniya yake ba! Hahaha. … Yauwa, to karɓi.

**Ali:** To na gode. Na ga harkar taka tana tafiya. Gaskiya yadda ka gyara rayuwark, da kuma yadda ka gyara wurin nan, kai, abin ya ba ni mamaki!

**Kawu Natanko:** Kai dai bari yaro, ina ɗan ƙoƙartawa dai!

**Ali:** To, amma ta yaya kuwa ka ƙwaci kanka daga matsalar cin bashi? Saboda na riga na san kana da matsaloli da yawa.

**Kawu Natanko:** Ai bayan matsalolin ma da kuma sarewa da rayuwa! Yunƙurawa na yi kawai na ƙuduri aniya canzawa. Amma babban abin dai shi ne, babarka da sauran abokan arziƙi su ne suka tallafa mini duk da kuwa cewa an ɗaure ni a kurkuku saboda na kasa biyan bashin da na ci da kuma

damfara da satar da na yi musu. Wannan hali nawa dai kam mummuna ne.

**Ali:** Ai duk na san abubuwan da suka faru a wannan lokacin. Amma kai kuwa wace hikima ka yi amfani da ita wajen canza irin wannan halin naka?

**Kawu Natanko:** Na samu shawarwari ne daga ƙwararru a lokacin da nake bursin. Abin da suke gaya mana shi ne: mu yi ƙoƙari mu dinga tafiyar da rayuwarmu daidai gwargwadon samunmu.

**Ali:** To kana ganin cewa tafiyar da rayuwarka daidai samunka zai sa ka rabu da cin bashi?

**Kawu Natanko:** Yin rayuwa daidai gwargwadon samunka ba yana nufin ba za ka ci bashi ba ne. Zan iya cin bashi don na bunƙasa harkokin kasuwancina!

**Kwastoma:** Kawu Natanko, ga kuɗinka!

**Kawu Natanko:** Tsaya, ina zuwa!

**Fitowa ta 2: A mashayar garin Kwazaye**

**Babawo:** Ke Maman Ladi, yau na ga duk kasala kike ji. Wai kin raina kuɗina ne ko?

**Maman Ladi:** Kai Babawo. Yau ma ka sake sato kuɗin matar taka ne don ka zo nan ka sha giya ko?

**Babawo:** To ai ko ma a ina nake samun kuɗin nan nawa, biya dai nake yi ko!

**Bash:** Ga zakin fa ya iso! Ke Maman Ladi, ba ni kwalbar giya ɗaya mana!

**Maman Ladi:** Kalle shi, kalli wannan kuma! Tun yanzu da sassafe har ka bugu? Sai ka biya ni kuɗin kwalba shida da ka sha tukuna, kana jina ko?

**Bash:** Ku ji wannan mata! Wa kike cewa ya bugu? Za ki ba ni kwalbar giya ko sai na …

**Maman Ladi** Sai ka yi me? Fita, fita ka ba ni waje!

**Bash:** Wallahi, ba inda za ni!

**Maman Ladi:** Au abin haka ne? To bari ka gani!

**Bash:** Kar ki matso kusa da ni! Ni fa gwanin kokawa ne idan ba ki sani ba. Ki bari fa na ce, zan...

**Maman Ladi:** Idan ka ji a jikinka ba sai mu ga gwanintar kokawar taka ba. Bari ka gani! Wofi kawai! …

**Fitowa ta 3: A wurin sayar da kayan marmarin Kawu Natanko**

**Ali:** Rayuwa ke nan! Allah Sarki Bash, kun ji fa irin yadda rayuwarsa ta kasance! Ba abin da yake, daga shiga wannan gidan giya sai ya shiga wancan, yana ta ɗirkar giyar kuma ba biya yake yi ba. Duk lokacin da ya samu kuɗi sai ya kashe su a kan giya!

**Kawu Natanko:** Kai wane irin mutum ne kai, kake ta magana kai kaɗai! Zancen me muke ɗazu ma? Yauwa na tuna, kana tambayata ne a kan yadda na daina cin bashi ko Aliyu?

**Ali:** E, so nake na ji daga bakinka. Kuma zai taimaka wa aikina, domin zan san yadda ake rayuwa a cikin bashi. Yanzu ni so nake ka gaya mini irin halin da ka shiga, da yadda aka kulle gidanka da ke cikin gari, da kuma yadda 'yan daba suka yi maka duka har ma a ƙarshe ka shiga kurkuku. Wai bayan waɗannan abubuwa shin za ka iya ba wani shawara ya ci bashi kuwa?

**Kawu Natanko:** Gaskiya in da hali, ya kamata mutum ya guji cin bashi! Amma fa cin bashi ba shi da wani aibu. Kai a matsayinka na jami'in bayar da bashi ka riga ka san haka. Kuskuren da mutane kawai suke yi wanda ni ma na yi irinsa shi ne, rashin mayar da hankali. Kuma mutum ya ci bashi saboda kawai ya ga kuɗi sakaka.

**Ali:** Kana nufin …?

**Natanko:** Ina nufin, bincike ya nuna cewa yawancin mutane suna da taurin bashi saboda sukan ci bashin ba tare da wani shiri ba takamaimai. Kuma idan suka samu kuɗin, sai su kashe su a kan abin da ba shi suka shirya wa ba.

**Ali:** Wato yanzu kana nufin ke nan cewa mutum ya dinga amfani da bashin da ya ciwo a kan abin da ya shirya?

**Kawu Natanko:** Haka ne, kuma da zarar mutum ya karɓi bashi kuma ya ji yana da 'yan kuɗi a hannunsa, to ya fara biya!

**Ali:** To wace shawara za ka ba wa masu matsanancin cin bashi?

**Kawu Natanko:** Idan har ka samu kanka kana cin bashi ne don shaye-shaye ko kuma caca, to ka yi maza ka nemi taimako! Za ka iya neman shawara daga wajen likita! Ko kuma wani da ka amince wa. Shawarar da za ta taimaka wajen fita daga ƙangin bashin domin kuwa ni ma ta taimaka mini! Sai dai ka sani fa cewa cin bashi yana da haɗari. Amma idan ka iya tsara abubuwanka, kasuwancinka zai bunƙasa.

**Bash:** Ka ga Kawu Natanko! Ka ga Kawuna na kaina!

**Kawu Natanko:** Kai wannan yaro! Yau ma dai a buge kake ko?

**Bash:** Kawu, ni ba a buge nake ba. So nake kawai ka ranta min Dala biyar zan biya ka kuɗinka gobe.

**Kawu Natanko:** Ni sai dai na ce ka sha lemo, zai fi maka alheri. Kuma ya fi giya.

**Bash:** Idan ba za ka ba ni kuɗin ba kawai ka faɗa. Bari ma na ɓace daga nan kafin ka ce za ka ba ni wani lemo. Lemo ai na yara ne. Ku ji wai ni ne ma zai ba wa lemo!

**Ali:** Kai ku tsaya! Wai wannan ba Bash ba ne?

**Kawu Natanko:** Wai kana nufin ba ka gane shi ba? Ai shi ne!

**Ali:** Bari ina so yin magana da shi. ... Bash! Bash! Tsaya mana!

**Bash:** Kai gaye, ƙyale ni ka ji. Ni ban san ka ba, kuma ba ka bina kuɗi.

**Ali:** Kai ni fa ba gaye ba ne! Ni ne abokinka Ali!

**Bash:** Bali?

**Ali:** Ni ne Aliyu Bello? Ko ka manta tare muka yi makaranta? Kai ƙaton kawai, har yanzu ba ka tuno ba?

**Bash:** Shege, Ali! Ni ne ka ce ma ƙaton kawai! Kai ba ga shi ka yi ƙiba ba! Amma na ji daɗin ganinka saboda na san yanzu kana son ka gayyace ni ne mu je mu ɗan sha wani abu a gidan shaye-shaye na Kwazaye ko?! Hakan kawai za a yi. Mu tafi kawai da Allah!

## Fitowa ta 4: A gidan sha na Kwazaye

**Bash:** Ehoho! Kyan tafiya dawowa!

**Mashayi na 1:** O'o! Kun ga gwanin ɗan kokawa ya sake dawowa!

**Maman Ladi:** Wai kai Bash ba ka ji abin da na gaya maka ba ne? Ba kai na gaya wa cewa kar ka kuskura ka ƙara dawowa nan ba tare da kuɗi ba? Fita ka ba ni waje!

**Bash:** Ke wannan matar me yake damunki ne?

**Maman Ladi:** Ni dai ina ƙara yi maka gargaɗi. Ina ƙara gaya maka kar ka kuskura ka bari na fito daga bayan kantar nan, wallahi sai ka yi kuka da kanka!

**Ali:** Shi ke nan, ya isa haka! Ni zan biya. Nawa kike binshi?

**Maman Ladi:** Dala 15!

**Bash:** Nawa?! Lallai wannan matar, rinto ma za ki yi mana? Dala 12 ne ba 15 ba!

**Ali:** Ya isa haka! Shi ke nan, na ce Bash! Ga Dala 15, karɓi!

**Maman Ladi:** To, ba ni!

**Bash:** To shi ke nan dai ko! Ba ga shi na zo da bankina na tafi-da-gidanka ba! Ke fa kin ɗauka ba zan biya ki ba ne, ko? Don Allah, kawo mana giya mu sha! Mu nan cike muke da kuɗi!

**Ali:** Ka ga, tsaya ka ji, Bash! Kwantar da hankalinka! Ina so gobe da safe ka zo kantin Kawu Natanko. Lokaci bai ƙure da za ka farfaɗo da rayuwarka ba! Kai dai ka zo gobe, amma fa a cikin hayyacinka! Ka ji ko?

**Bash:** To, Ali!

**Mai ba da labari:**
Bash, Bash! Ai ba zai yiwu a ce duk ƙwazon da yake da shi ya bi ruwa ba! Na san cewa mutum ne shi mai wayo da dabara, kuma na san zai zo goben. Kuma zan taimaka masa domin kuwa da ma abin da ya kamata a ce abokai na yi wa juna ke nan!
To masu saurarenmu, wannan dai matsalata ce ba taku ba domin kuwa mun zo ƙarshen wannan wasan kwaikwayo namu wanda James Muhando ya rubuta. Idan kuna son sake jin wannan jerin shirye-shirye, sai ku ziyarci shafinmu na yanar gizo wato dw.de/lbe. Za kuma ku iya tuntuɓarmu a shafinmu na 'Facebook'. Ku huta lafiya.

**’Yan Wasa:**

Shehu Ali Shagari

Buhari Ibrahim

Maryam Mohammed Ibrahim

Habiba Inuwa

Zainab Bala

Munir Isa

Ɗan Fulani

Yunusa Musa

Mercy Shekari

Huraira Ibrahim

Bulus John

Ruƙayya Bala

Neeta Yusif

Kabiru Mohammed

Zainab Ibrahim

Ado Muhammed

Lola Abdulkadir

Yusuf Idris

Zainab Abubakar